Lallai cewa Annabi ya aika Wani Mutum a wani yaki sai ya kasane yana" karantawa abokansa in yana jansu Sallah, Sai yake cika karatunsa da: Kulhuwa.

Daga Nana Aisha -Allah yarda da ita- "allai cewa Annabi ya aika Wani Mutum a wani yaki sai ya kasane yana" karantawa abokansa in yana jansu Sallah, Sai yake cika karatunsa da: Kulhuwa"

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim suka Rawaito shi]

Annabi -Tsira da aminci Allah su tabbata a gareshi- ya wakilata wasu daga Sahannabnsa a kan wata Rundunar yaki, don Jagorantar ta da kuma yin hukunci a tsakaninsu, kuma don kada abin ya zama babu tsari, kuma ya zabi wanda ya fi kowanne Addini da Ilimi da kuma iya tafi da yaki, shi yasa Shugabannin sune Limamai a cikin salloli, kuma su suke bada Fatawa sabida Iliminsu da Addininsu, to sai ya rika karanta musu Kulhuwa a kowace Rakao'i biyu na kowace Sallah; sabida sonsa da Allah da kuma sunayensa da sifofinsa, kuma duk wanda yaso Allah to zai yawaita ambatonsa, to yayin da suka dawo daga yakin nasu zuwa ga Annabi sai suka gaya masa abinda ya faru sai ya cce ku tambayae shi mai yasa yake yi sai suka tambayeshi mai yasa yake yin hakan haka kawai yake yi ko kuma sabida wani abu ne? sai Jagoran nasu ya ce: ina yin haka ne Sabida ta kunshi sifofin Allah don haka nake son Maimaita ta sai Annabi ya ce ku gaya masa kamar yadda ya ke maimaita wannan sura saboda soyayyarsa da ita; kuma sabida abinda ta kunsa na sifofin Allah masu girma wanda wannan Surata kunsa na Sunayensa da aka ambata, to shima Allah yana sonsa, kai wannan ta isa falala.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/5213